Wanda yake so a yalwata masa a arzikinsa, kuma a jinkirta masa a rayuwarsa, to, ya sadar da zumuncinsa

Daga Anas ɗan Malik - Allah Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - ya ce: "Wanda yake so a yalwata masa a arzikinsa, kuma a jinkirta masa a rayuwarsa, to, ya sadar da zumuncinsa".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - yana kwaɗaitarwa a kan sa da zumuncin 'yan uwa ta hanyar ziyara da girmamawar jiki da dukiya da makamancin hakan, kuma cewa su sababi ne a yalwatar arziki da tsawon rai.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5372